# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al'umma a Afirka
## Kashi na biyu: Cimma buri cikin sauƙi


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Adams: | ɗan shekara 10 |
| Jammo: | ɗan shekara 45 |
| Hadiza: | 'yar shekara 30 |
| Shusha: | ɗan shekara 50 |
| Fati: | 'yar shekara 16 |
| Tanko: | ɗan shekara 45 |
| Dauda: | ɗan shekara 40 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan cin zarafi a nahiyar Afirka. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda Jummai ta tafi ta bar ƙawarta Hadiza ita kaɗai a bakin rijiya inda suka saba ɗebo ruwa, da kuma yadda Hadiza ta ɓoye a cikin wani kogo a lokacin da wasu 'yan ta'adda suka zo wurin da take. Me zai faru bayan nan? Za mu kuma waiwayi Fati, yarinyar nan 'yar shekaru goma sha shida da haihuwa da ta fara karatu a makarantar kwana ta maza da mata. Sannan kuma za mu ji yadda Adams za su ƙare da sabon kawunshi Jammo bayan mahaifiyarshi ta gabatar da shi a wurin Adams. Sai a biyo mu don jin abubuwan da za su kasance a cikin wannan shiri na biyu.

Yanzu bari mu faro daga wurin yaron nan Adams wanda uwarsa ta bar shi a hannun kulawar Kawu Jammo.

**Fitowa ta 1: A gidan su Adams**

**Jammo:** Adams, sukarin da ka sa ya yi yawa. Sai ya yi maka lahani. … Kai! Ba na ce maka ya isa haka ba! Kai wane irin yaro ne!

**Adams:** Nan fa gidanmu ne! Kuma ina iya yin duk abin da na ga dama.

**Jammo:** Saurare ni ka ji Adams, ban san abin da mahaifiyarka ta faɗa maka ba. Amma ni ba zan iya jure irin wannan halin naka ba.

**Adams:** Saboda haka ai sai ka tafi! Ai da ma ba wanda ya ce ka zo nan.

**Jammo:** Yaro ka iya bakinka. Ni ba mahaifiyarka ba ce da ke ƙyale ka.

**Adams:** Sannan kuma kai ba babana ba ne! … Aaah! Ka tafi ka bar mana gida! Na tsane ka! Ka tafi!

**Jammo:** Shi ke nan! Ya isa haka! Kuma sai na koya maka hankali!

**Adams:** Bari Mamana ta dawo gida! Sai na faɗa mata ka duke ni.

**Jammo:** Ba abin da za ka faɗa mata! Kuma idan har ka faɗa mata sai na yanke maka harshenka, kuma in gutsura maka waɗannan ƙananan kunnuwan naka. Ka gane ko? Adams, na ce ka gane ko?

**Adams:** Aaaah! Wayyo Allahna! Wayyo Allah!

**Mai ba da labari:**
A yawancin lokuta cin zarafin mutum yana farawa ne da sa tsoro a zuciyarsa saboda ta haka ne wanda yake son cin zarafin yake samun damar yin yadda yake so. Sai a sa wanda ya shiga wannan hali ya kasance ba shi da wani abin da zai iya, ko za ta iya yi, sannan kuma shi mai cin zarafin, ko kuma su masu cin zarafin sai su samu damar cin karensu ba babbaka. A halin da ake ciki yanzu wanda ya kamata ya kare Adams daga wani hatsari, ko wasu da za su cutar da shi, shi ne yake neman cin zarafinshi ta hanyar duka.
Kafin mu kai ga jin abin da zai faru, bari mu waiwayi Hadiza a bakin kogi inda take ta yin addu'ar cewa Allah ya sa 'yan ta'addan nan waɗanda wani mai suna Shusha yake wa jagoranci ba su gan ta ba.

**Fitowa ta 2: A rijiya**

**Hadiza:** Oo ni Allah, ga su nan zuwa! Kuma nan suka nufo! Wayyo ni Allah, za su kashe ni!

**Shusha:** Yoohooo! Malama, sannunki sauraniya, kina jiran yarimanki ne ya zo? Ai sai ki sa wa kanki ruwa don kuwa ga shi nan ya iso! Amma ba a kan doki ba, a'a. Mu a nan a-kori-kura ce muke da ita, kuma cike da maza mayunwata.

**Hadiza:** Wayyo! Don Allah kar ku kashe ni, kar ku kashe ni don Allah! Ina roƙon ku! Don Allah ku ƙyale ni in tafi, ban yi muku kome ba.

**Shusha:** Wa ya ce zai kashe ki? Eh? Kai, ku fito da ita daga cikin kogon nan.

**Hadiza:** Kar ku zo kusa da ni, kar ku zo kusa da ni! Wa zai taimake ni? Don Allah wani ya taimake ni!

**Shusha:** Don Allah ku rufe mata bakin nan! Ba na so in ƙara jin ihun nan. Zo nan! Yauwa, haka ya fi. To yanzu tun da ni ne shugaba, ni zan fara da ita.

**Mai ba da labari:**

Fyaɗe dai wani abu ne da kowace mace take tsoro. Sannan kuma mafi tashin hankali shi ne a ce rukunin maza sun yi wa mace ɗaya fyaɗen. Akwai labarai na mata da yawa da aka yi wa fyaɗe, ko aka wulaƙanta su a wuraren yaƙi. Allah Sarki, yanzu Hadiza ta shiga cikin rukunin irin waɗannan matan. Kamar sauran matan da suka shiga wannan halin na fyaɗe ta yi duk wani abin da za ta iya yi, amma ta gagara. Bai kamata a ce wani ya zargi wadda ta shiga irin wannan halin ba saboda ba wanda ya san halin irin waɗanda abin ya shafa suke ciki. A cikin wannan halin Hadiza ta yi iyakar ƙoƙarinta. Sau da yawa ta yi ta yakushi da shure-shure don ta ture mazajen da ɗaya bayan ɗaya suka wulaƙanta ta. Tana faɗin ceton ranta da kuma ɗan da ke cikin cikinta, amma

daga ƙarshe sai ƙarfinta ya ƙare, ta kasa ci gaba da yin komai don ta kare kanta. Duniyar duk ta rufe mata, ta kasa sanin ko ina take, ko kuma ita wace ce, ko har tsawon wane lokaci hakan 'yan ta'addan za su ci gaba da yi a kanta. Ba ta ma san lokacin da suka ɗauki motarsu suka tafi ba. Hadiza tana matuƙar zubar da jini. Ta kasa jure wa zafin da take fama da shi. Tana ta tunanin ko mutuwa za ta yi. Wannan tunanin sai ya sanyaya mata zuciya. Shin wani zai gano ta da wuri kuwa? A ci gaba da sauraronmu.
Amma yanzu bari mu koma makarantar kwana ta su Fati, inda take ɗaya daga cikin sabbin yaran da suka fara karatu a nan. Yanzu shugaban ɗakin kwanan ɗalibai, wato Malam Tanko, ya kira ta zuwa ofishinsa.

**Fitowa ta 3: A ofishin Malam Tanko a makaranta**

**Tanko:** Shigo.

**Fati:** Sannu Malam Tanko. Ka ce kana nemana?

**Tanko:** Aha! E, Fati! Shigo ki zauna. Ki rufe ƙofa mana. Yauwa! To zauna mana, zauna, zauna! Kar ki ji tsoron komai, ba laifi kika yi ba.

**Fati:** To Malam, na gode.

**Tanko:** Kar ki damu. To, yaya karatu?

**Fati:** Lafiya lau.

**Tanko:** Kuma ɗakin kwanan da aka ba ki ya yi miki kuwa? Gadonki ya yi miki?

**Fati:** E ya yi, ba wata matsala, Malam. Na gode ƙwarai da gaske.

**Tanko:** Kuma ba wanda yake ba ki matsala ko? Kin san muna jin maganganun cewa manyan ɗalibai suna matsa wan a ƙasa da su.

**Fati:** A'a! Sai dai ma yadda kowa yake neman ya taimaka min.

**Tanko:** Kin tabbata? Kar ki ji tsoron faɗa mun idan wani yana matsa miki. Ki tuna fa cewa ke amana ce a hannuna.

**Fati:** Na gode, Malam.

**Tanko:** To su kuma… mmh… mazajen fa?

**Fati:** Hm?

**Tanko:** Na ce su yara mazan da ke makarantar fa. Haba Fati! Na tabbata cewa wasu daga cikinsu suna damunki. Kin ga ke sabuwar zuwa ce, sannan kuma ga shi ke yarinya ce ƙarama kuma ga ki kyakkyawa, kuma… kuma irin abin da suke so ke nan.

**Fati:** Yallaɓai, ban fahimci abin da kake nufi ba.

**Tanko:** Shi ke nan. Mu bar wannan maganar. Amma dai ki tuna, in har kina da wata damuwa, to ki zo ki faɗa min. Kina iya wucewa yanzu.

**Fati:** To Malam, sai an jima.

**Tanko:** To madalla. Saurara, akwai wani abu ɗaya. Za ki iya riƙe mini sirri?

**Fati:** To… ya danganta…

**Tanko:** Ba wani abu ba ne can, na umurci *captain* ɗin ɗakinku da ta ba ki sabuwar katifa. Amma kar ki faɗa wa kowa. Wannan wata dama ce da ɗalibai ƙalilan ne kawai suke samunta.

**Fati:** Tooo… to na gode, Malam.

**Mai ba da labari:**

Yana da wuya a yarda da abin da yake faruwa, amma maganar gaskiya ita ce Malam Tanko yana nuna wa Fati sha'awa ne. Ku tuna fa, shekarunta goma sha shida kacal, sannan kuma ɗalibarsa ce. Yana kan wani babban matsayi ne, kamata ya yi kuwa a ce ya nuna mata hanyar arziki, kuma yana ilimantar da ita. Yana ƙoƙarin ba Fati wata dama ta musamman, yana ƙoƙarin ya bambanta ta ne da sauran ɗalibai mata. Shin za ta iya kauce wa wannan tarkon da ya kafa mata kuwa?

A halin da ake ciki kuma a can ƙauye Dauda yana ta jiran matarsa Hadiza ta dawo daga ɗiban ruwa. Da ya ga har dare ya yi ba ta dawo ba sai ya shiga cikin damuwa. Sai Dauda ya tafi wajen ƙawar Hadizan, wato Jummai, wadda a ko da yaushe tare suke tafiya ɗiban ruwa.

**Fitowa ta 4: A gidan su Jummai**

**Jummai:** Kai wannan yaro! Yaya kake so in yi da kai ne, Audu? Haba, ɗana, yi shiru mana!

**Dauda:** Sallama dai. Ina wuni, Jummai.

**Jummai:** A'a, Dauda, ka ba ni tsoro! Me ya sa ba ka ƙwanƙwasa ƙofar ba?

**Dauda:** Yi haƙuri Jummai. Ba da gangan na yi ba. Ina neman matata ce, Hadiza.

**Jummai:** Hadiza? Ban… ban gane ba. Ba ta gida?

**Dauda:** A'a. Shi ya sa ma na zo nan. Tare kuka tafi ɗiban ruwa da ita. Shi ya sa nake tunanin ko kin san inda take. Tun tuni nake ta jiranta, kuma yanzu ga shi na shiga matuƙar damuwa.

**Jummai:** To, ni dai a bakin rijiyar na bar ta. Kuma tun lokacin ban gan ta ba.

**Dauda:** Kin bar ta a can? Ita kaɗai? Me ya sa? Ba tare ya kamata a ce kun dawo ba?

**Jummai:** E, amma zan biya wurin goggota ce da ba ta da lafiya don in kai mata ruwa. Amma kar ka samu damuwa, Dauda. Na san cewa ba abin da ya same ta. Wataƙila ita ma ta kai ziyara ne wani wurin.

**Dauda:** A'a! Dole ne in shiga cikin damuwa. Kin san tana da juna biyu! Zan je bakin rafin na duba ta. Hadiza ba ta daɗewa a waje ba tare da ta dawo gida ba. Wannan ba halinta ba ne.

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, da haka kuma muka kawo ƙarshen wannan shiri na yau. Me Dauda zai yi idan ya ga matarshi cikin halin da take ciki? Ku tuna dai cewa 'yan ta'adda ne suka yi wa Hadiza fyaɗe, kuma har yanzu tana can a some a bakin rijiyar kusa da rafi. Sannan, waɗanne irin dabaru ne Malam Tanko zai ci gaba da yi wa yarinyar nan Fati?

Duk waɗannan da ma sauran ƙarin bayanai za su zo muku ne a cikin

shirinmu na gaba. Kafin nan kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Ko kuma mu haɗe da ku a shafinmu na Facebook don aiko da saƙwanni ko kuma muhawara. Sai mun sadu a shiri na gaba. A huta lafiya.